# SUNNAH NEWS NIGERIA

## Labaran Sunnah A Tafin Hannun ku

**MUJALLAR SUNNAH DOMIN SANIN HALIN DA SUNNAH KE CIKI** *DATE: Friday 22, December, 2017*

## SHUGABAN KASA MUHAMMADU BUHARI YA GANA DA SHUGABAN IZALAR NAIJERIYA

Shugaban kasa Muhammadu Buhari ya gana da Shugaban IZALAR Naijeriya Sheikh Abdullahi Bala Lau, da Sheikh Kabiru Gombe, da Sheikh Yakubu Musa Hassan Katsina da Sheikh Dr. Ibrahim Jalo Jalingo a fadar gwamnatin Najeriya ASO ROCK a yammacin Talatar wannan mako.
Ganawar wacce ta Dauki kusan mintuna 160, sun tattauna muhimman batutuwa wadanda za su ciyar da kasa gaba Insha Allah.
Muna addu’ar Allah ya sanya albarka acikin wannan ganawa ya kuma kawo kasarmu cigaba.
Allah ya kara girma da daukaka Sheikh Bala Lau, Allah ya bada lada.

**Rahoto: Basheer Sharfadi Kano**





### ‘YAN AGAJIN KUNGIYAR IZALA BAKWAI (7) SUN RASA RAYUKAN SU A KANO

Anyi jana'izar yara matasa Yan Agaji guda bakwai ( 7 ) daga cikin ‘yan agajin kungiyar Izala na jihar Kano sakamkon wani mummunan hadari da suka samu akan hanyarsu ta dawowa gida daga taron bita da bangaren agaji na kungiyar ya gudanar a karamar hukumar Kibiya dake nan Kano, domin koyar dasu yadda zasu inganta aikinsu na addini da taimakon al'umma, alokacin da akayi hadarin mutum biyar suka rasu, a kan hanyar su ta zuwa asibiti daya ya kara rasuwa bayan anje asibiti sai aka kara samun mutum daya ya rasu.
A takaice dai Mutum bakwai suka rasu wanda yanzu haka da akwai wasu ‘yan agaji dake kwance a asibiti wasu basusan ma inda kansu yake ba, da safiyar yau ne shugaban kungiyar Izala na Jihar Kano Dr. Abdullah Saleh Pakistan ya jagoranci jana'izar wasu daga cikin mamatan, daga bisani kuma yaje yayiwa iyayen Mamatan ta'aziya har gidajen sugu.
Babban abin da ya bani sha'awa shine duk gidan da Dr. Pakistan yaje domin yi musu ta'aziya sai kaga mahaifan yaran duk da alhinin da yake ciki na rashin dansu amma abin kai kace alfahari suke suna alfahari da wannan shahadar da yayansu sukayi sukace su abin Alfahari ne a wajensu saboda yayansu akan harkar Addini suka rasa ransu.
Muna Addu'a Allah ya karbi shahadar wadan nan bayin nasa Allah ya musu Rahama Su kuma iyayansu Allah ya basu hakurin rashin yayansu.

**Rahoto:** ***Abdullahi Suraj Nagegeme***

**Sabuwar Tashar Sunnah News TV Tana Kan Hanya**

**A yanzu** dai tuni dandalin Sunnah News yayi nisa wajen samar muku da sabuwar tashar talabijin wadda zaku iya samu a wayoyin ku, ana saran fitowarta cikin mako mai zuwa.

Darulfirk.com Takuce Domin Yada Sunnah
Cibiya guda daya tilo wadda take kawo muku karatuttukan maluman Sunnah daga wurare daban-daban a kowane lokaci, aciki da wajen kasarmu Nigeria.
http://facebook.com/darulfikrng

# Ana Sanyawa Yara Sunan Sahabi Mu'awiya (R.A) A Sokoto

A yanzu haka al'ummar musulmi na Sokoto na ci gaba da sanyawa yayansu maza da Allah ya basu sunan babban sahabinnan Mu'awiya Ibn Abu Sufyan Allah ya kara yarda agareshi, acikin makon nan ma a unguwar hubbaren shehu Dan Fodiyo ma, wani bawan Allah mai suna WADATA LOKI ya sakawa dansa jariri suna Mu'awiya, hakan na kara nuna mana cewa da'awar sarkin kogo ta neman rufe hasken ... Mu'awiya a idon musulmi bai yi nasara ba.

Hakan ya tuna mani da abinda ya faru a shekarun baya (2005) a sokoto lokacin da rikicin shi'a da musulman gari yayi kamari duk sunan da za'a saka idan namiji ne za'a sa masa Abubakar , Umar ko Usman, idan kuma mace ce za'a sa ka mata Aisha ko Hafsa Allah ya kara yarda da su.

Tarihi dai shine ke maimaita kansa, bayan haka babban limamin Masallacin Malik Anas kuma Garkuwan sahabbai ahlul baiti da waliyai Asheikh imam Nuraddeen Nata'ala Hausare yayi alkawalin cewa idan aka sake yi masa haifuwar da namiji zai saka masa suna Mu'awiya Allah ya kara mana son sahabi Mu'awiya radiyallahu anhu.

Rahoto: ***Hussain Auwalu Ya'u***



## DAGA MASALLATAN JUMU'AR MU




**Shiri ne dake kawo muku jigon sakonnin hudubobin jumu'a da aka gabatar a masallatan jumu'a daban-daban a ciki da wajen kasarnan, shiri ne da Ammar Isah Nuhu Batagarawa ke shugabanta tare da taimakawar Basheer Journalist Sharfadi, Shiri ne da yake da dimbin masu sauraro sannan zaku dinga jin halin da duniyar musulunci ke ciki a kowane mako ta cikin shirin, zaku iya samun wannan shiri da ma wadanda suka gabata a kowane lokaci a www.darulfikr.com**

**Domin daukar nauyi ko tallata hajar ku ta cikin shirin, ko kuma aiko da taku hudubar sai a tuntubi: 08035830253, 08066989773, 08149332007, dagamasallatanmu@gmail.com http://facebook.com/masallatanmu.ng**

### Shugaban Izala Yakai Ziyara Ofishin Shugaban 'Yan Sanda Ta Kasa, (Igp)

Tawagar kungiyar IZALA ta kai ziyara ofishin shugaban 'yan sanda ta kasa, (IGP) a birnin Abuja,kuma shugaban rundunar 'yan sandan ta kasa ya karrama Sheikh Abdullahi Balalu Bala Lau, musamman akan tarurruka da yake shiryawa wadanda suka shafi kawo zaman lafiya a kasa.

Rahoto: **Ammar Isah Nuhu**



### Mataimakin Gwamnan Jihar Yobe Ya Gina Makarantar Marayu A Potiskum

Mataimakin gwamnan jihar Yobe ya gina gidan marayu a karamar hukumar Potiskum,

Gidan marayun mai dauke da makaranta da wurin kwanan dalibai, mataimakin gwamnan Injiniya Abubakar D. Aliyu yace ya gina makarantar ne da kudin aljihunsa.

Rahoto: Hassan Auwalu



### Izala Taje Kudancin Nigeria Don Jajantawa Wadanda Rikici Ya Shafa

Sheikh Abdullahi Bala Lau ya turo tawagar ne musamman domin duba Makaranta da Masallacin da aka rusa a garin ILESHA dake jihar Osun, da kuma Zuwa Jajantawa yan uwa a garin ILE-IFE dake jihar Osun abisa rikicin a watan 3 shekarar 2017.

Tawagar ta hada da Daraktan Agaji na kasa Engr. Mustapha Imam Sitti wanda yagoranci tawagar sai Sheikh Imam Khidir Manufa Zaria, Sheikh Aliyu Telex... Sheikh Mas'ud Offa, Mal. Aliyu Kwara, Mal. Auwal Gulama, da kuma Mal. Sani Direba.

Allah yahuta gajiya kuma yasaka da mafificin Alkhairi.

Rahoto: **Hussain Auwalu Ya'u**



# Cikakken Tarihin Sheikh Dr. Sani Umar Rijiyar Lemo

## An Bude Makarantar Sheikh Ja'afar Mahmud Adam College of Islamic And Arabic Studies A Garn Tsafe Na Jihar Zamfara

A cikin wannan makone ne aka bada sanawar bude katafiyar makaranta a garin Tsafe na jihar Zamfara makarantar ta kunshi dukkan bangarorin boko dana addini. Hakanan kuma ta kunshi dalibai maza da mata.
Za'a iya samun Form din a wurin Sakataren makarantar Mal. Nafi'u Labaran ko Malama Rabi'atu M. Ma'aruf a harabar makarantar dake kusa da gidan Wamban Tsafe, Tashar 'yar hanne, hanyar Asibiti. Kudin Form N1,000 kacal.
Za a iya samun su ne da misalin karfe 2 zuwa 5 na ranakun Litinin, Talata, Laraba, Alhamis, da Asabar. Domin karin bayani 07069252241, 07035975014

Rahoto: ***Hashim Surajo Tsamiya***

Cikakken sunan sa shi ne Muhammad Sani bn Umar bn Musa Rijiyar Lemo. An haife shi a 1st July 1970, a birnin Makka na kasar Saudi Arabia.
Yayi kuma kuruciyarsa ne a unguwar kofar mata dake birnin Kano, Nijeriya. Malam yayi Firamarensa a makarantar Khairul Bariyya Islamic Primary School Kano (1978-1983). Sannan yaci gaba da karamar sakandire (H.I.S) a sakandiren Shahuci Kano (1987), kuma ya wuce Government Arabic Teachers College Gwale in da ya kammala babbar sakandiren (Senior Islamic Studies) da darajar Distinction a shekarar 1989. Dr Muhammad Sani ya samu gurbin karatu a tsangayar ilmin hadisi ta jamiar musulunci ta Madina in da ya kammala digirinsa na farko (B.A. in Hadith Science and Islamic Studies,1994) da digirinsa na biyu (M.A.in Hadith Science and Islamic Studies, 2000) dukkanninsu ya fita da darajar (Excellent).



Bisa sha'awarsa ta ilmi mai zurfi da bincike, malam ya zarce da karatun digirinsa na uku a nan jamiar musulunci ta Madina wanda Allah ya bashi damar kammalawa a shekarar 2005, da darajar (Excellent and first class upper). Malam yayi karatun littafai masu yawa a wajen malamai da dama a nan gida Nijeriya da kuma Saudi Arabiya, wadanda suka hada da, Malam Hamza Adakawa (Akhdari, Arbauna hadisan, Ishriniya, Hamziyya da sauransu), Mal. Sani Inuwa (Nahwu da Sarfu), Mal.Mahbub Abdulkadir Sumaly (Balaga), Mal. Bashir Hasan (Adab), Mal.Aminu Mahe (Tarikh). Daga cikin malamansa na saudiyya kuwa akwai:- Sheikh Abdulmuhsin Al-Abbad (Tauhid), Sheikh Ali Abdurrahman Alhuzaifi limamin Madina (Tauhid), Sheikh Abdulaziz Abdullatif (Jarh Wattaadil), Sheikh Muhammad Matar (Tadwin and Ruwat), Sheikh Dr. Hafiz Alhakami (Musdalahul hadis), Sheikh Dr.Muhammad Nur Saif (Musdalahul hadis), Sheikh Dr.Abdussamad Abid (Musdalahul hadis), Sheikh Dr. Umar Hawiyya (Tafsir) da Sheikh Dr. Faihan Almudairi (Fiqh). Malam ya halarci tarurrukan karawa juna ilmi da kwasa-kwasai da dama a nan gida Nijeriya da kasashen Saudi Arabiya, Sudan.
Rahoto: ***Hassan Auwalu Ya'u***

## An Kashe Mutum Goma A Masallacin Gamboru

Wani dan kunar bakin wake ya kai hari wani masallaci a garin Gamboru da ke jihar Borno a arewa maso gabashin Najeriya.
Dan kunar bakin waken ya badda kama ne ya shiga cikin masallaci, ya tayar da bam dinsa a lokacin da ake sallar Asuba.
Shaidu sun tabbatar wa BBC cewar harin ya kashe mutum goma ciki har da maharin.
Kawo yanzu dai babu wanda ya dauki alhakin kai wannan harin, sai dai kuma shugaban wani bangare na kungiyar Boko Haram, Abubakar Shekau, ya yi barazanar kai wasu hare-hare a wani bidiyon da ya fitar ranar Talata.
Rahoto: ***Muhammad Habib Adam***

## Dr. Usman Giade Ya Kammala Digirinsa Na Uku

Alaramma Usman Giade ya samu nasarar kammala Digiri na uku a kasar Sudan!!!
Gabanin haka ya rubuta Qura'ani da hannunsa daga kuma kwanyarsa sau da dama.
Kai dai abune na zamani Amma ai rubuta Qur'ani sau daya ya fi zama Dr Zamani!!!
Alaramma sai a koma tsangaya a ci Gaba da Satu!!!
Ya kammala da First Class!!

Rahoto: **Basheer Journalist Sharfadi**



## An Kaddamar Da Taron Bita Akan Ayukkan Yan Agajin Jibwis Na Kasa Baki Daya A Gusau

A ranar Alhamis 4-1-2018 ne aka kaddamar da taron bitar littafin aikin agaji ga masu horar da aikin agaji na tarayyar nigeria a garin Gusau da munufar kara inganta ayukkan su.
Da yake jawabi a wajen buda taron bitar, Mataimakin daraktan agaji na Kasa mai kula da Bada Horo da Ayukka na Yan agajin Izala na Kasa baki daya, Malam Muhammad Kabir Saidu Gusau yace makasudin gudanar da bita shine a horas da masu koyar da aikin agaji bai daya, domin su bada irin horon bai daya ga sauran yan gajin da ke karkashin kulawar su a sauran jahohi. Yana mai cewar taron bada horon har ila Yau zai bada damar sanin juna don kulla zumunci tsakanin sauran yan uwa daga jahohi mabanbanta daga ciki hadda yan agaji daga Jamhurivar Niiar.

Daga nan sai Mal. Kabir Gusau ya shawarci malarta taron da su jajirce don su koyi aikin ta hanyar maida hankali da kuma gabatar da tambayoyi akan ababen da suka shige masu duhu na aikin agaji Wanda ake yi don taimakon addinin musulunci badon kudi ba saboda idan kowa ya koma jahar daya fito ya cigaba da karantar da sauran yan agaji bai daya.
Malam Muh'd Kabir yayi kira ga resu su zama masu jin tsoron Allah da ladabi da biyayya hadi da tsabta, domin nasarar ayukkan su, ya kuma karanto tarihin agaji tare da gabatar da addu'o'i ga yan agajin da suka rasu kamar su Aliyu Funtua wadanda suka bada gudumawa wajen ganin an tsabtace aikin na Agaji.

Rahoto: **Abdullahi Salisu Faru**

## Babban Limamin Izala Na Jos Ya rasu

Allah yayiwa Sheikh Ridwan Dahir Abubakar Jos rasuwa a daren alhamis dinnan bayan gajeruwur jinya a wani asibiti dake birnin Jos a Naijeriya, kafin rasuwar sa shine Babban Limamin JIBWIS a Jos,
Sannan na kusa ga Marigayi Sheikh Dr. Alhassan Sa'id Adam Jos, kuma daya daga cikin Malaman Kasa, za'a gabatar masa da Janaza da misalin Karfe 8:00am na safe a kofar gidansa, kusa da gidan Alh. Idris Mai kaset a unguwar kofar 'yan kwaba a cikin birnin Jos insha Allah.
Allah ya jikan sa da rahama, ya kyautata makonci, tare da sauran musulmai Muminai. Amin.

Rahoto: **Ammar Isah Nuhu**

## Maluman Sunnah Biyu Da Sakatarorin Jibiwis Social Media Biyu Sun Angwance A Wannan Makon

A wannan makon da muke ciki ne maluman Sunnah guda biyu suka angwance wadanda suka hada da Dr. Jamilu Zarewa fitaccen marubuci kuma manazarci wanda ke zaman na gaba-gaba cikin masu da'awa musamman a shafukan sadarwa na zamani, sai kuma Mal. Abubakar Abdussalam wanda aka fi sani da Baban Gwale wanda daya ne daga cikin limaman wannan cibiya ta **Sunnah News Nigeria** kuma sakataren kwamitin samina na kungiyar Izala ta kasa, sannan malami mai karantarwa kuma mai da'awa,
A gefe guda kuma an daura auren sakatarorin Jibwis Social Media na jihohin Kano da Kuma Sokoto, Lawal Mamman Bilbis daga Kano, sai Alaramma Filabri Garba, muna fatan Allah ya sanya musu albarka aciki amin.
Rahoto: ***Basheer Sharfadi Kano***

# SASHEN TALLA

## Izala Zata Gabatar Da Wa'azin Jiha A Gusau

Alh. Aliyu Na Allah Zurmi, Shugaban kungiyar Jama'atu Izalatil Bidi'ah Wa Iqamatis Sunnah na jaha.
Sheikh Sirajo Muhammad Gusau, Shugaban majalisar Malamai na jaha.
Alh. Musa Haruna Kwaren Ganuwa, Daraktan agaji na jaha.
Amadadin kungiyar Jama'atu Izalatil Bidi'ah Wa iqamatis Sunnah ta jahar Zamfara na farin cikin gayyatar yan uwa Musulmai wajen saurarон wa'azin jaha wanda kungiyar ta saba gabatarwa ko wane wata.

Za'a gabatar da wa'azin ne ranar Asabar 18/4/1439AH dai dai da 6/1/2018, za'a gabatar da wa'azin a Shiyyar Mareri da ke garin Gusau. Za'a fara wa'azin da karfe 4:00 na yamma har zuwa illa masha Allah.

Sanarwa: **Abdullahi Salisu Faru**

## Izala Zata Gabatar Da Wa'azi A Garin Maradun

Alh. Abubakar Aliyu (Dan madamin Maradun) Shugaban Jibwis Maradun
Mal. Haruna Sulaiman, Shugaban majalisar Malamai na Maradun.
Mal. Rabi'u Sulaiman, shugaban 'Yan Agaji Maradun
Amadadin kungiyar Jama'atu Izalatil Bidi'ah Wa iqamatis Sunnah ta Maradun, na farin cikin gayyatar yan uwa Musulmai zuwa wajen sauraron wa'azi, wanda kungiyar zata gabatar a garin faru.
**Za'a gabatar da wa'azin ne ranar Jumu'ah 17/4/1439 - 05/1/2018.**
**Za'a fara wa'azin da karfe 4:00 na yamma har zuwa illa masha Allah.**

Sanarwa: **Abdullahi Salisu Faru**

## Za'a Gabatar Da Daura Ta Kwana Daya A Potiskum

**Ana sanar** da 'yan uwa daliban ilmi cewa za'a gabatar da daura ta kwana daya a garin Potiskum daurar wadda za'a gabatar kamar haka:
**Rana:** Talata 22-04-1439 = 09-01-2018
**Wuri:** Masallacin tunawa da Sheikh ja'afar Mahmud adam wanda akafi sani da Masallacin Gada
**Lokaci:** 9:00Am zuwa 04:30pm
**Masu Gabatarwa:**
Sheikh Dr. Adam Usman Nangere da Dr. Yawude
**Take:** *Ilmin Rabon Gado*
**Kudin Shiga:** ₦500 kacal,
Idan an gama za'a baiwa kowa certificate, ana samun form din a masallacin daga safe har zuwa dare.

## ZA'A GABATAR DA MUHADARA A KANO

Ana gaiyatar al'ummar musulmi zuwa gagarumar lakca, wacce za a gabatar kamar haka:
Maudhu'i: Sahabbai da matsayinsu a gurin duk wani muminin kwarai, daga Kur'ani da Sunnah
Malami mai gabatarwa: Sheikh Shehu Mansur Dala
Malamai masu ta'aliki:
1)- Sheikh Kabir Bashir Abdul Hamid, (Hayaki fidda na kogo)
2)- Sheikh Muhammad Bin Usman Kano
Ragowar Manyan malamai sun hada da
1)- Dr. Kabir Muhammad Kofa
2)- Dr. Muhammad Muslim Ibrahim
da sauran manyan malamai
**Rana**: JUMA'A (5/1/2018)
**Lokaci:** Magrib zuwa Issha'i
**Wuri:** Masjidus Sahaba, Kundilar Zaria Road, Kano.
Allah ya bada ikon zuwa.

Sanarwa: **Muhd Habib Adam**



**SUNNAH NEWS NIGERIA –DOMIN AMFANUWAR MUSULMAI**
Ku biyo mu ta: http://sunnahnewsnigeria.wordpress.com http://facebook.com/sunnahnigeria.ng
http://twitter.com/sunnahnigeria 09035830253, 08066989773, 08149332007, 08168015170

# DAGA KASASHEN WAJE

## Musulman Kasar Jamus Sun Gabatar Da Wa'azi Da Kuma Sada Zumunci

A duk karshen shekara Musulmi 'yan asalin Afirka mazauna Jamus kan hadu don sada zumunci a tsakaninsu tare da gudanar da wa'azi da laccoci don fadakar da juna koyarwar addini tare da gudanar da liyafar cin abinci.

Da karatun na Al-qur'ani mai girma ne a ka bude taron na bana da ya gudana a garin Oberhausen na jihar Nordrhein Westfalen wanda ya samu halartar Musulmai daga sassan kasar ta Jamus da ma wadanda suka halarci taron don saurararon wa'azi daga bakin malamai da suka gabatar da wa'azi da ya mayar da hankali wajan fadakar da al'ummar bukatar tashi tsaye wajen rike koyarwar addinin Islama bisa koyarwar Qur'ani da Hadisan ma'aiki (S.A.W).

Taron an shirya shi ne a karkashin inuwar kungiyar al'ummar Musulmi ta kasar Jamus, wacce aka fi sani da "Muslim Umma in Germany". Kungiya da ke aiki don hada kan al'ummar Musulmin 'yan asalin nahiyar Afirka mazauna Jamus.

Abdulmumin Yahaya Abbas wanda ke daya daga cikin malamai da suka gabatar da wa'azi a taron ya bayyana cewa duba da yadda Musulmai musamman 'yan asalin Afirka basu da rinjaye a kasar ta Jamus na daga cikin dalilai na shirya wa'azin a lokutan hutu don tunatar da mabiya koyarwar addinin.

Shiekh Sulaiman shi ne babban limamim masalacin Masjudul Sunnah a birnin na Oberhausen, ya bayyana cewa baya ga wa'azin da kungiyar ta faro yau shekaru talatin, ana kokari na ci gaba da yada addinin a sauran sassa da ma gina wuraren ibadu.


Yayin Wa'azin Kenan A Jamus

## Jam'iyyar Netanyahu Ta Amince Wa Yahudawa Su Ci Gaba Da Mamayar Yankunan Falasdinawa

Jami'iyyar Likud da Firaministan Isra'ila Benjamin Netanyahu ke wa jagoranci ta amince da wani kudirin doka da ya halastawa Yahudawa su ci gaba da mamayar yankunan Falasdinawa da ke Yammacin Gabar Kogin Jordan.

A cikin kudirin an yi kira da Isra'ila ta mayar da yankunan da ta mamaye nata a hukumance tare da yin sabbin gine-gine a yankuna da suka yi wa kaka-gida.

Ministoci 'yan jam'iyyar Likud sun amince da kudirin duk da cewa, ba su da alaka da shi.

Bayan an gabatarwa da majalisar dokoki kudirin za a tattauna kan batun.

Ana bukatar yin zama sau 3 kafin a amince da dokar.

## Mutum 10 Sun Mutu A Zanga-Zangar Kasar Iran

Mutane 10 ne suka mutu sakamakon zanga-zangar da jama'ar Iran suke yi saboda tsadar rayuwa a kasar.

Sanarwar da tashar Talabijin din Iran ta fitar ta ce, ana ci gaba da rasa rayuka sakamakon zanga-zangar da aka fara a ranar Alhamis din makon da ya gabata a tsakiya da yammacin kasar.

An bayyana cewa, ya zuwa yanzu mutane 10 ne suka mutu inda sama da 200 suka jikkata.

Sakamakon yadda gwamnati ba ta sano zanga-zangar ta yadu ta katse hanyoyin sadarwar yanar gizo.

Ana zanga-zangar ne sakamakon rashin aiyukan yi da matsin rayuwa da al'umar Iran ke ciki.

## An Ba Da Fatawar Haramta Kudin Intanet, Bitcoin

Babban malamin addinin musulunci na kasar Masar, Shawki Ibrahim Abdel-Karim Allam, ya fitar da wata fatawa inda ya haramta amfani da kudin intanet na Bitcoin. A fatawar da a ka wallafa ranar Litinin, Shawki Allam ya ce ba a yarda musulmai su siya ko su siyar ko kuma su biya haya da wannan tsari na Bitcoin ba.

Ya ce amfani da kudin intanet na da hadari domin zai iya haifar da zamba da yaudara, kuma kasancewar tsarin maras tabbas, ya na iya cutar da jama'a da ma kasashe.

Babban malamin ya ce sai da ya nemi taimakon masana tattalin arziki kafin ya yanke wannan hukunci.

Bitcoin na da abubuwa biyu da suka bambanta shi: kudin intanet ne kuma ana ganinsa a matsayin wani abu da za a iya amfani da shi a madadin kudi.

Kudin yana kan intanet sabanin kudaden takarda ko sulalla da ke aljihunka

Duk da cewa akwai wasu na'urorin bayar da kudi (ATM) na musamman da ke bayar da Bitcoin, ya fi dacewa a yi tunaninsu kamar 'yan kudaden intanet. Kuma babu gwamnati ko kuma bankin da ke buga Bitcoin.

Wannan na nufin "ba kudin da doka ta amince da shi ba ne, ba za ka iya biyan harajinka ko kuma ka yi amfani da shi wajen biyan bashi ba", in ji Dr Garrick Hileman na fannin koyar da kasuwanci a jami'ar Cambridge.

Ana samar da Bitcoins ne ta wata hanya mai sarkakiya da ake ce wa "haka" (wato "mining, a Ingilishi), sannan wasu komfuntoci da ke hade a fadin duniya za su saka ido kansa.

Ana samar da kimanin Bitcoin 3,600 a ko wace rana – kuma a halin yanzu akwai kimanin kudin miliyan 16.5 da ke yawo.

Sai dai kuma, kamar dukkan kudade, darajarsa ya dangata ne ga iya kudin da mutane suke son saye shi tare da sayar da shi.

## An Kashe Wani Musulmi A Indiya Don Ya Hana Sa Waka A Sabuwar Shekara

An yi wa wani musulmi dukan kawo wuka har sai da ya bakunci lahira a Jharkhand da ke gabashin Indiya, bayan da ya bukaci wasu mutane su kashe wakar da suka kunna ranar sabuwar shekara.

Al'amarin dai ya faru ne a Mandar, wani gari a kusa da birnin Ranchi.

A ranar Talata ne mutane suka rufe wata hanyar mota don nuna bukatarsu ta kama wadanda suke da hannu cikin lamarin, sai dai 'yan sanda sun tarwatsa dandazon mutanen.

An kara tura wasu jami'an 'yan sanda yankin, don tabbatar da zaman lafiya tsakanin Musulmai da kuma al'ummar Hindu.

Waseem Ansari mai shekara 19, yana aikin leburanci ne a Pune kuma ya dawo kauyensu ne kwana biyu da suka gabata.

## Yawan Musulmai Zai Kara Karuwa A Amurka

An bayyana cewar yawan Musulmi a Amurka za su ninka a cikin shakarar 2050. Ganin yadda Musulmi ke kara hijira zuwa Amurka ya sanya wasu tambayar ainihin yawan Musulmi a kasar yanzu.

Hukumar binciken PEW da ke Amurka wacce ke gudanar da bincike akan addinai a duniya ta bayyana cewar: Bisa ga binciken shekarar 2017 yawan Musulmin Amurka yakai miliyan 3.45, hakan na nuni da kashi 1.1 na al'umar Amurkan baki daya. Haka kuma hukumar ta yi hasashen cewa yawan Musulmin zai fiye na Yahudawa a kasar a cikin shekarar 2040, a wannan shekarar Musulmi za su kasance addini na biyu mafi yawa bayan addinin Kiristanci a Amurkar.

Hasashen hukumar ya kara nuna cewa a shekarar 2050, yawan Musulmin zai karu zuwa miliyan 8.1, ya kuma kasance da kaso 2.1 cikin dari na al'ummar kasar.